KARATU BANDA KUKA

MOORE THEOLOGICAL COLLEGE LIBRARY
3 2042 00098028 8

S.P.C.K.

Moore

MOORE COLLEGE LIBRARY

Presented by

From the library of

A. Capell

493.72 HAU

Moore College
Library

KARATU BANDA KUKA

[FIRST READER—HAUSA]

LONDON
SOCIETY FOR PROMOTING
CHRISTIAN KNOWLEDGE

Moore College
Library

078516

Made in Great Britain

KARATU BANDA KUKA

a b ḅ ch d ḍ e f g h

i j k ḳ l m n o p r s

sh t u w y z

a e i o u

BABI 1

ba ta ga da ma sa da wa ka
za na pa fa sha ya ja an am

n a g a p a.
w a y a b a k a?
z o y a b a t a.
y a k a, k a s h a.
w a z a y a s a k a?
a m b a t a t a s h a.
b a t a d a ḍ a b a.
n a b a t a, b a t a s h a b a.

BABI 2

ban ran man chan jan
shan zan kan ḍan yan
nan gan pam bar har
yar yas sa'a ba'a
nan-da-nan

nan ka bar ta?
ya kan ba ta ta sha.
ran nan za ya ba ta.
ban ba ta sa'a ba.
na yas da sa'a chan.
zan ba ḍan man-ja.
ka bar ta fa, za ta chan.
sa'an nan an ba ka?
sa'an nan na gan ta chan.
da ya ba ka, ka sha nan-da-nan.

Moore College
Library

BABI 3

b a - d a	y a - n a	w a - ḳ a	m a - n a
n a - m a	r a - w a	k a - z a	t a - n a
ḅ a - t a	k a - m a	r a - n a	k a - f a
w a - s a	m a - s a	n a - s a	t a - ḅ a
n a - t a	n a - w a	d a - w a	h a - k a
k a - d a	t a - s a	m a - t a	t a - r a
ḳ a - s a	y a - f a	k a - s a	t a - b a
k a - r a	y a - r a	s a - r a	ḳ a - r a
f a - d a	t a - k a	B a - l a	a m - m a
	K a - k a	k a - y a	

an ba ta jan tasa.
am ba ta pam tara.
ana saran dawa.
na gan ta nan, tana da dawa.
ban taḅa ba ta ba.
Bala ya ḅata dawa.
yana da nama da kaza.
ta bada man-ja ga Kaka.
na bar ta chan, tana rawa.
ya kan kama kaza da rana.
zan kafa nawa a nan.
Bala ya ba ta nasa, amma ta sha nawa.
yana waḳa amma ba ya san waḳan ba.
tana wasa tana rawa chan.
yana bada ḳara ga yara.
an ḳara mata kaya.

BABI 4

f i j i n i y i m i b i s h i
k i c h i ḳ i i n j i n y i n
b i n k i n c h i n ḳ i n i - r i
i - d i I - b i b i - r i F i - b i
k i - ḍ i m i - j i f i - l i j i - k i
j i - b i K i - r i r i - m i s i - s i
s h i - r i c h i - k i n

ga bi-i, ga shi chan.
ran nan ban chi ba, ban sha ba.
kin ba ni sisi.
ba ta da miji.
kin kama kifi? ki ba ni nan.
tana chin kifi; ba ta ji ki ba.
ki bi shi, har ki kama shi.
Kiri tana wasa, ta ḳi ta ji ki.
bar ni in ji waḳan nan.
kin ji kiḍi? ban taḅa jin irin-shi ba.
yana da kifi iri iri.
Fibi tana chikin dawa.
tana wasa a fili.
an chi kifi chikin Idi.
Kiri ta yi shiri.
tana rawan jiki.
jibi za a sara rimi.
an yi masa ba'a.

BABI 5

je ke ne che ke-ḅe
le-le ḍe-be ke-ke se-ye
ke-re le-ḅe ne-me ge-fe
je-re che-che

ya kere nama.
ya cheche shi.
ga kifi, na seye shi.
ya gan shi, ya keḅe shi.
ya ba shi keke.
je ka, ka ḍebe shi daga chan.
minene wan-chan? keke ne.
wan-nan keke nawa ne.
kazan chikin dawa ta ke.
je ki, ki kama wata kaza.
wan-nan tasa tata che.
ba ni ne ba; ke che.
na neme ta, amma ban gan ta ba.
an kama kada a gefen nan.

BABI 6

s u d u k u m u
m u n s u n k u n d u k

m u - t u m u - s u h u - ḍ u r u - h u
N u - h u h u - t u k u - d u g u - d u
u - k u k u l - l u m

mu je mu gan shi.
kaza ta mutu.
sun yi mata musu.
kullum ku yi haka.
zan fada ma Nuhu.
sun kama kifi uku.
tana hutu har sa'a huḍu.
Nuhu yana da ruhu.
sun yi shiri za su kudu.
Bala ya sha duk.
yan kaza sun mutu.
kun yi rawa amma ba ku yi waḳa ba.
Nuhu ya gudu amma na kama shi.

BABI 7

	k o	s o	t o	z o
n o - n o	r o - ḳ o	r o - g o	g o - r o
f o - r o	k o - m o	k o - r o	k o - k o
k o - g o	D o - g o	ḳ o - ḳ o	g o - y o
s o - s o	t o - r o	t o - z o	y o - y o
	z o - m o	s o - r o	

ku zo mana, ku ba ni nono.
ba ni so su ba ni goro.
mun komo daga kudu.
Dogo ba shi da foro.
sun sa goro chikin kogo.
ya zo, ya yi roḳo mu ba shi keke.
ku ba ta ḳoḳo ta sha.
Dogo ya yi koko; mun sha.
su sun sa rogon nan, ko ba haka ba?
to, ki bar shi.
ya zo daga Ibi.
ka zo zan goyo ka.
soro yana yoyo.
an ba ni soso da tozo.
zomo ta gudu chikin kogo.
an koro toro nan.

BABI 8

ma-yas ka-man Al-lah ka-dan zam-na
bab-ba Ad-am ba-yan sam-ma ba-har
pan-sa ḳam-na han-ya wan-da a-ba-da
Ta-lata ma-da-ra da-ya-wa ka-ma-ta
sa-la-ma La-ra-ba sa'an-da ma-ga-na
na-sa-ra ta-ta-ra ha-ka-nan sa'an-nan
yan-ma-ta wa-ḍan-nan ma-ka-ran-ta
ḳan-ḳa-na-na

ran Talata ya ga makaranta.
na bada madara dayawa.
waḍannan yanmata sun zo ran Laraba.
ya kamata mu yi waḳa ga Allah.
kadan ka ji magana ka zo nan.
da kaka yara ḳanḳanana za su sara dawa.
Allah ya ba mu babbar salama.
bayanda ya gan ka, sa'annan ka yi shi hakanan.
akan ran Talata na yi nasara.
na ga kada a gefen bahar.
da na ḅata wannan hanyar, na neme ta.
ḳaḳa za mu tatara su duk, mu mayas da su?
ya Allah wanda kana chikin samma har abada.
ka ji mu.

Moore College
Library

BABI 9

mu-tum mu-gun hun-tu gun-tu ḍun-gum
shu-ru tu-tur su-kur kur-ku-ku ru-bu-tu
bu-tu-lu ku-tu-ru mu-zu-ru ru-ku'u kun-ku-ru

an sa mugun mutum chikin kurkuku.
da, yana huntu, am ba shi kwakwata,
amma butulu ne shi.
ka gaya masa ya yi shuru ḍungum.
kuturun ya mutu a Jos,
Nuhu yana da ḍan kunkuru.
Mamman ya yas da guntun sandassa.
Laraba ta ba muzuru kifi.
an saya masa sukur dayawa.
nan gaba za mu yi waḳa ga Allah kullum.
ya kamata mutum shi yi ruku'u gaban
Allah kullum.

BABI 10

jir-gi gin-di gir-bi gir-ki ki-shi
kir-ki ḳi-shi ḳir-ji ni-shi sir-di
sil-ki sit-tin i-na gi-shi-ri jin-ji-ri
jin-ki-ri li-ti-ni

Mamman jinjiri ne.
Jibi, Kiri za ta ba Fibi sisi.
matansa tana ma goyon jinjiri.
mun yi jinkiri, mu zo da jinjiri.
na gan shi chan, yana hutu a
gindin rimi.
ina jin ḳishi, zan sha koko.
jibi za a sara rimi a gindin.
ga kuturu chikin jirgi, yana nishi.
mugun mutum ya kan yi kishi.
ran Litini za mu yi girbin dawa.
ina so gishiri in yi girkin nama.
an ba ni sisi in yi girkin kifi.

BABI 11

gw-and-a gw-am-ma gw-al-gw-ad-a
gy-aḍ-a gy-ar-a gy-ar-ta

Bala ya ba ni gwanda.

malam za ya zo ran Litini ? ko gwamma Talata ne ?

Fibi tana chin gyaḍa.

an ba ni man-gyaḍa.

ka zo ka gyara mani jirgin nan.

soro yana yoyo, ka zo ka gyarta.

Martha tana da gwanda da gyaḍa.

na sa man-gyaḍa chikin tasa; za a gyarta keke da shi.

BABI 12

kw-a kw-a-ḅa kw-a-la-ba kw-a-na ḳw-an-ḳw-a-sa
kw-an-ta ḳw-a-ya kw-a-tan-ta

ita kwa ta gan shi.
ya kwaḅa ḍanyar ḳasa.
ta sa kwalabar madara a kanta.
kwana tara ya zamna chan.
ana ḳwanḳwasa a sakata.
Bulus ya zo, ya kwanta a ḳasa.
kaza ta chi ḳwayar dawa.
shi Matta ne ? ni kwa ban san shi ba.
Yusufu za ya kwana nan.
Hajara, sa' anda ki ji ana ḳwankwasawa,
nan-da-nan ki zo.
da mi za mu kwatanta wannan magana ?

BABI 13

ts-ab-ta ts-a-da ts-a-ka ts-a-ra ts-a-ts-a
ts-a-wa ts-a-ya ts-o-ro ts-i-bi-ri ts-ar-ka-ka

tasan nan ba ta da tsabta.
ayaba tana tsada a loton nan.
Bulus ya sa kaya a tsaka ga jirgi.
ga keken Yusufu, tsatsa ta ḅata shi.
da yamman nan mun ji tsawa.
yana chikin tsere, aka tsayadda shi.
jirgi yana chan a gefen tsibiri.
Yahaya yana tsoron ḍan-sanda.
ba zan ji tsoron dufu ba.
Allah za ya tsabtadda mu.
tsarkaka za su ga Allah.

BABI 14

Allah yana ḳamnarmu.

Bulus ya zo daga Filibbi

Ḃarna ka ke yi.

Chan chikin bahar an bar shi.

Dawa ba ta yi ba.

England tana da makaranta dayawa.

Fibi tana wasa a fili.

Garba ya zo, ya ba ni goro.

Hawa tana rawa akan hanya.

Ibi, ban taḃa gan shi ba !

Jirgi yana da kaya dayawa.

Kaka ta yi; bar mu yi girbin dawa.

BABI 15

Ḳamna ba ta jin kishi ba.

Laraba za ta mayas da tasa.

Malam ya tattara yara chikin makaranta.

Nuhu ya ji maganar Allah.

Oho ! Ban san ta ba.

Pataka dayawa ta tattara don ta yi chiniki da su.

Ran Litini za mu fara makaranta.

Salama, Allah kwa shi ba mu.

Tabarma tana nan amma ba ta da tsabta.

Uwatasa ta mutu, tun yana jinjiri.

Wawa yana wasa a fada.

Yanmata sun yi shiri don makaranta.

Zomo ya zamna chikin dawa.

BABI 16

ru-wa	go-ma	sa-mi	gi-da	ḅe-r a
su-na	ko-wa	da-wo	fi-to	ḳe-ta
ku-ra	go-na	sa-me	bi-yu	che-to
du-ba	ko-gi	ta-fi	ḍi-ba	de-na
ku-sa	do-ya	da-re	shi-ga	ge-mu

Ḅera ta chi dawa da dare.

Tsofon mutum yana da gemu.

Kowa ya yi ḳeta ta komo kansa.

Cheto daga Allah ya ke.

Ba za mu dena yin yaḅo ga Ḍan Allah ba.

Ta tafi, ta shiga chikin gida, ta sami doya, ta ḍiba guda biyu, ta fito.

Ya tafi gona, kusa da kogi; kowa ya san shi.

Ga ni, na dawo, ban same shi ba, na tafi na duba har so goma, ban gan shi ba.

Kura ta kan zo da dare, ta sha ruwa; mu fa, muna jin tsoro.

Ga ruwa dayawa chikin kogi; da ḳyar na shigo gari.

BABI 17

li-ta-fi	Al-ha-mis	mu-ta-ne	da-mi-na
Ju-ma'a	tu-fa-fi	da-ḍe-wa	fi-ti-la
lo-ka-chi	mi-sa-li	mu-ri-ya	ka-su-wa
al-he-ri	ka-ra-tu	zu-chi-ya	gas-ki-ya
sa-bi-li	ru-bu-tu	han-ḳu-ri	du-ni-ya

zu-nu-bi Al-ma-si-hu fa-rin-chi-ki

Ran Alhamis mu kan yi karatu, ran Juma'a kuma mu kan yi rubutu chikin litafi.

Tun da daḍewa annabawa su kan ji muriyar Allah.

Mutanen duniya ba su san gaskiya da alheri ba.

Babu misalin ga hanḳurin Allah.

Almasihu ya zo duniya sabili da mu.

Mutanen duniya su kan yi zunubi tun daga farko;

Amma yanzu za su yi farinchiki domin Isa Almasihu ya cheche su.

Yara suna koyon karatu chikin makaranta, amma idan ba su koyon gaskiya kuma, makaranta ba ta daḍe masu komi ba.

Ka sayo mani fitila da tufafi a kasuwar.

Lokachin damina chiwon zuchiya ta same ta.

BABI 18

s-ai k-ai d-ai kw-ai r-ai w-ai m-ai
mai-bi mai-magani mai-koyaswa mai-b-ai-wa
mai-sh-ai-da l-ai-fi k-ai-fi h-ai-fi g-ai-da
r-ai-ra l-ai-ma w-ai-yo sh-ai-tan
t-ai-ma-ko k-ai-to f-ai-fai d-ai-dai

Waiyo ! Ta yi wani babban laifi.
Wai, Wai, Wai ! Ban taḅa jin yara da raira waḳa irin wannan ba !
Yanzu lokachin damina ne; ba zan tafi majami'a banda laima ba.
Ita, mai-koyaswa za ta zama; kai fa, mi za ka yi ?
Ta tafi kasuwa domin ta sayi faifai da mai, da kwai, da wuḳa mai-kaifi.
Mai-magani mutum mai-baiwa ne, kullum ya kan bada taimako.
Im ba mu sami taimako daga wurin Allah ba, sai Shaitan ya yi nasara da mu lallai.
Daidai ne mai-bin Isa ya zama mai-shaida da mai-koyaswa kuma.
Maryamu ta haifi ḍanta, sunansa Isa ne; mutane suka tafi suka gaishe shi.

BABI 19

y-au h-au l-au y-au-wa b-au-ta ḅ-au-re
B-au-chi d-au-ḍa y-au-she ḍ-au-re ḍ-au-ki
g-au-ta h-au-ka z-au-re H-au-sa h-au-shi
ḳ-au-ye n-au-yi r-au-ni s-au-ra s-au-ḳi
t-au-sa-yi

Yaushe za mu komo Zaria ?
Ita ta dauri zani mai-tabshi.
Bari mu hau itachen ḅauren nan, ya fi sauḳi.
Yauwa ! Yau za mu Bauchi; a wani loto za mu tashi ?
Tana lafiya lau amma ta tafi ḳauye garin samun gauta.
Yana zaure, ya kan ḍauki kaya mai-nauyi, amma ana chewa yana hauka.
Yana jin haushi; wani ya zo ya kawar masa da sauran itachen.
Ta ji Hausa amma ba ta iya yin magana da Hausa ba.
An yi masa rauni, dauḍa kwa ta shiga chikin miḳin, yanzu shi abin tausayi ne.
Ya kamata mu ḍaukaka Allah, mu bauta masa kuma.

BABI 20

na-si-ha fa-ha-ri-ya kum-bu-ra han-ka-li
cha-ku-na nu-ku-ra a-dil-chi jim-re-wa
dau-re-wa ḳa-re-wa ban-gas-ki-ya

Ḳamna tana da yawan hanḳuri,
Tana da nasiha;
Ḳamna ba ta jin kishi ba;
Ḳamna ba ta yin fahariya,
Ba ta yin kumbura,
Ba ta yin rashin hankali,
Ba ta bida ma kanta,
Ba ta jin chakuna,
Ba ta yin nukura;
Ba ta yin murna chikin rashin adilchi,
Amma tana murna da gaskiya;
Tana jimrewa da abu duka.
Tana gaskanta abu duka,
Tana kafa bege ga abu duka,
Tana daurewa da abu duka.
Ḳamna ba ta ḳarewa daḍai.

BABI 21

Yah-weh ma-ki-ya-yi-na ru-wa-ye hu-ta-wa
war-tsa-kad-da han-yo-yin ha-ki-ka tsa-ki-yar
i-nu-war ko-wa-che ke-ren-ka ta'az-i-ya
table ḳwa-ri-yar kwa-ni-kin jin-ḳai

Yahweh makiyayina ne; ba zan yi rashi ba.
Yana sanya ni in kwanta a chikin makiyaya maiḍanya:
Yana bishe ne a gefen ruwaye na hutawa.
Yana wartsakadda raina.
Yana bishe ni a chikin hanyoyin adilchi, sabili da sunansa.
Hakika, ko tafiya ni ke yi ta tsakiyar kwari na inuwar mutuwa,
Ba zan ji tsoron kowache mugunta ba, gama kana tare da ni:
Sandarka da kerenka suna yi mani ta'aziya.
Ka kan shiriya table a gabana a idanun maḳiyana:
Ka shafe kaina da mai; ḳwariyar shana ta chika har tana zuba.
Nagarta da jinḳai kaḍai za su bina dukan kwanakin raina:
Za ni zamna kuma a chikin gidan Yahweh har abada.

PRINTED IN GREAT BRITAIN BY BILLING AND SONS LTD., GUILDFORD AND ESHER

Moore College
Library